# Ko Yaushe Za'a Kammala Titin Jakara-Goron Dutse?

Daga Maryam Hassan Abba

Tsohon gwamnan jihar Kano kuma sanatan Kano ta tsakiya Engr. Dr. Rabi'u Musa Kwankwaso shi ne ya ga dacewar canjawa wannan titi mai hannu daya suna daga Jakara-Goron Dutse zuwa sunan wani babban malamin addini da ake kira Sheikh Mahmoud Salga. Bayan canja suna kuma sai ya ga yiwuwar mayar da titin hannu biyu ta hanyar biyan diyya ga gidajen da za'a iya tabawa a lokacin aikin, sannan kuma a sanya masa fitilu don haskaka hanyar. Yin titin zai rage cunkuson da ake yawan samu na ababawan hawa a kusan kowane yammaci a hanyar, musamman wajen dadaddiyar bolar Jakara mai tsawon tarihi. Hakan kuma zai kara dauke bolar da ta dade tana illata mutanen da suke zaune a kusa da gurin ta wajen sanya musu cutuka mabanbanta, musamman zazzabin cizon sauron da bolar ke taimakawa wajen kawowa.

Zancen nan da nake maka tsawon shekara shida kenan har yanzu ba'a iya kammala hanyar da bata kai tsawo kilomita biyu ba. Tun a shekarar 2012, shekara daya bayan hawan tsohon gwamnan aka fara wannan aiki amma har yanzu da nake wannan rubutu ba'a iya kammalawa ba. Hasalima dai an bar aikin kuma an dauke kayan aikin sama da shekara biyu da ta wuce. Gwamna Abdullahi Umar Ganduje shi ne ya gaji aikin daga tsohon gwamnan da ya yiwa mataimaki a tsakanin shekarar 2011 zuwa 2015. Aikin an bayar da shi ga Hukumar Gyaran Hanyoyi ta Jihar Kano (Kano Road Management Agency, KARMA) saboda titin dan karami ne da ba sai gwamnati ta nemi wasu yan kwangila na daban ba. Amma zancen nan da nake maka babu aikin babu ma'aikatan. An bar mazauna kusa da gurin suna shakar kura cikin duhu.

Cikin wani irin abu mai kama da kokarin bayyana an gama aikin da ko rabinsa ba'a yi ba, Gwamna Abdullahi Umar Ganduje ya bayyana a safiyar wata rana da

tawagarsa ya ce ya bude titin! Abin da zai baka mamaki shi ne ko birji ba’a gama zubawa a karkashin tarin kasar da take sanya cutar “athma” a titin ba. Hanyar ta zamo wata babbar illa ga tarin al’ummar da suke zaune a hanyar da kuma masu gangarowa zuwa tsohuwar kasuwar Kurmi dake jihar Kano. Bayan cakwalkwalin da hanyar take bayarwa a lokutan damuna, cunkuson hanyar ya kara mata abin haushi da duk wanda yake biyo hannu dayan da shi kadai ne masu kekuna ke wucewa cikin salin-alin. Masu mota da baburan Adaidaita Sahu kuwa jijjiga kadai ta isa mai cikin wata tara ta haihu ko mai karamin ciki tayi bari. Duk a irin wannan halin gwamnati ta debe kayan aikin titin kuma ta bayyanawa rediyo cewa ta bude titin!

Wani abin mamaki da takaici kuma shi ne tuni aka gama biyan diyyar gidajen da aka rusa kofofinsu a hanyar amma har wasu gidajen na yunkurin dawo da abin da aka tashesu da shi. Hanyoyi da magudanan ruwa a toshe suke musamman a lokacin damuna. Duhu kuwa shi ne alamar hanyar matukar yammaci ya karato saboda rashin fitulun titi. Wannan ta janyo masu kwacen waya da masu mummunan hali suna labewa a gurin don su samu mafaka. Da irin wannan yanayi na hunturu kuwa ya zama haramiya mutum ya sanya kaya masu kyau ba tare da baci ba. Masu ciwon tarun fuka da “athma” kuwa sai rashin lafiya ce ke dada karuwa.

Ina son na yi amfani da wannan dama wajen kira ga mahukunta da gwamnati akan su yi wa Allah su duba wannan hanya da aka barta bayan an fara yinta mai muhimmanci da ta hanyar ake bi a tafi kasuwar Kurmi don karfafa tattalin arzikin jiharmu. A hanyar akwai makarantun firamare da na Islamiyya a kalla guda goma da yara suke bi da fararen kaya. Sannan hatta ruwan fanfon da yake gangarowa daga hukumar bayar da ruwan sha ta WRECA zuwa unguwannin Jakara, Aikawa, Musukwani, Mararraba, Yalwa, Chediya da sauran unguwanni kusan guda goma duk ta hanyar yake biyowa. Tun bayan fara wannan hanyar rabon da yan wadannan unguwa su samu ruwan sha na fanfo cikakke ko da na sati guda ne.